# Ya Manzon Allah, shin kana ganin idan wani mutum ya zo yana son karɓar kuɗina?

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Wani mutum ya zo wurin Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - sai ya ce: Ya Manzon Allah, shin kana ganin idan wani mutum ya zo yana son karɓar kuɗina? Ya ce: «Kada ka ba shi kuɗinka)) Ya ce: Shin kana ganin idan ya yaƙe ni? Ya ce: «Ka yaƙe shi» Ya ce: Shin kana ganin idan ya kashe ni? Ya ce: «Kai shahidi ne». Ya ce: Shin kana ganin idan na kashe shi ? Ya ce: «Shi yana cikin wuta»

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Wani mutum ya zo wurin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - sai ya ce: Ya Manzon Allah, shin kana ganin idan wani mutum ya zo yana son ƙwatar dukiyata? Ya ce: Bai wajaba ka miƙa wuya ka ba shi dukiyarka ba, ya ce: Shin kana ganin idan ya yaƙeni? Ya ce: Yana halatta gareka ka yaƙe shi, ya ce: Shin kana ganin idan ya kasheni fa? Ya ce: To kai shahidi ne, ya ce: Shin kana ganin idan na kashe shi fa? Ya ce: Shi ya cancanci a yi masa uƙuba a cikin wuta a ranar alƙiyama.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/3557